# BISHARA TA HANNUN MARKUS

Marubuci : Malam Fred Morris




## Sashi na fari :

## Ga qalibi ko mai bi da bincike

Fassarorin nan suna bayyanar gaskiyar Maganar Allah a Hausa mai sauxin ganewa. Ka iya binciken Littafi Mai Tsarki da taimakon littattafan nan ko a gida ko tare da abokai. Idan taron bincike ne, ya fi kyau kowane qalibi yana da littafin nan na kansa duk da Littafi Mai Tsarki.

Duk inda ka ga alamar '☞ **ka karanta**', sai kullum kai ko shugaban taron ya karanta nassin Littafi Mai Tsarki wanda aka ambata, sa' an nan ka cigaba da karatun fassarar littafin nan.

- Sashin '**Yi magana a kan wannan**' yana da tambayoyi waqanda za su nuna ko qalibi ya fahimci ayoyin Littafi Mai Tsarki. Tambayoyin nan gwadawa ne.
- Akwai kuma tambayoyi inda za ka zapi amsa mafi kyau. Za su ba ka tunani a kan karatunka. Mun ba ka amsoshin tambayoyin nan a xarshen littafi.
- Sashin '**ka xara karatu a Littafi Mai Tsarki**' yana da muhimmanci. Allah zai yi magana da kai ta wurin nassoshin nan. Saboda haka sai ka nemi dukan ayoyin da aka ambata, ko a cikin taron ko daga baya a gida. Waqansu daga Tsohon Alkawari ne, ana kiransu kuma 'Rubutacciyar Maganar Allah'. Shi ne sashin Littafi Mai Tsarki wanda aka rubuta kafin zuwan

© Fred Morris, Manna Publications

# MARKUS YA BA DA LABARI MAI DAQI A KAN YESU ALMASIHU

Bishara ta hannun Markus, ko Labari Mai Daqi ta hannun Markus, shi ne littafi na biyu daga cikin huqu a kan rayuwar Yesu Almasihu. Wani saurayi mai bi, sunansa Yohanna Markus, ya rubuta littafin nan wajen 42 zuwa 44 AD (wato, AD yana nufin shekarar da aka haifi Almasihu). Bitrus ya gaya masa abubuwa da yawa game da ayyukan Yesu da koyarwarsa. Waqannan abubuwa suka faru a xasar Yahudiya da xasar Galili, waqanda yanzu muna kira Xasar Isra ' ila. Littafin Markus ya gaya mana da yawa zancen rayuwar Yesu a mako na xarshe kafin a haqa shi da gicciye da xusoshi ya mutu. Xarshen littafi ya ba da labarin tashin Yesu da rai, da komawarsa Sama shi kasance tare da Ubansa Allah.

Bisharar Markus sura 1 zuwa 8 suna ba da labarin farkon aikin Yesu, da koyarwarsa da warkarwar da ya yi. Labari Mai Daqi shi ne Allah yana xaunarmu, har ya aiko da Qansa Yesu domin ya mutu dominmu. Shi ya sa dukan mutane ko ' ina waqanda suke sujada ga Allah, suna gaskata da Yesu kuma, suna da rai madawwami tare da shi.

# WANENE MARKUS?

Yohanna Markus Bayahude ne, amma an fi saninsa da sunan Markus wanda ke sunan helenanci. Ya koyi da yawa daga Bitrus almajirin Yesu. Bitrus ya xaunaci Markus, har ya kira shi Aqana (1 Bitrus 5:13). Mahaifiyar Markus tana da babban gida a Urushalima, babban birnin xasar Isra'ila, wanda a dâ xasar Yahudiya ce. Ta ji Labari Mai Daqi a kan Yesu Almasihu, ta kuma ba da gaskiya. Kirista sukan taru a gidanta domin sujada da addu'a (Ayyukan Manzanni 12:12).

Mafi yawan shugabannin addini suna da almajirai da mutanen da suke barin aikinsu domin su bi shugaban, su koya daga gare shi. Markus ya bi Bitrus, wanda ya bi Yesu. Ya saurari maganar Bitrus game da Yesu, a kan abubuwan da Yesu ya yi da kuma ya faqi. Saurayin nan Markus ya gaskanta cewa Yesu Almasihu ne. (Azancin sunan Almasihu da Kiristi duk qaya ne.)

Markus da Barnaba kakansu qaya ne, Barnaba kuma abokin Bulus ne. Markus ya yi tafiya tare da Bulus da Barnaba domin su ba da Labari Mai Daqi a Asiya Xarama (wato, Xasar Turquie a yau). Amma ya tashi ya bar su, ya koma gida Urushalima. Bulus bai so ya qauki Markus a tafiyarsa ta yaqa bishara ta biyu ba. Saboda haka Barnaba ya qauki Markus tare da shi, suka tafi Sayifurus (Kubrus). Daga baya, Bulus da Markus suka sake kama abuta. Lokacin da yake cikin

**Abubuwa 20 waqanda Rubutacciyar Maganar Allah ta ce a kan Yesu cikin Tsohon Alkawari (TsA) da yadda suka cika a cikin Sabon Alkawari (SA)**

1. Yesu ne Almasihun da aka alkawarta, Qan Allah. (TsA: Maimaitawar Shari ’a 18:15; Irmiya 23:5; SA: Matiyu 16:16; Markus 1:11; Luka 2:11)
2. Yesu ne Mai Ceton duniya wanda aka alkawarta. (TsA: Ishaya 53:12; SA: Luka 2:11; Ibraniyawa 7:25)
3. Yesu ne Mai Warkarwa wanda aka alkawarta. (TsA: Ishaya 35: 5 - 6; SA: Markus 2:12; 7:35; 8:25)
4. Asalin Yesu gidan Sarki Dawuda ne. (TsA: Ishaya 9:7; SA: Matiyu 1:1)
5. An haifi Yesu a Baitalami ta xasar Yahudiya, a cikin kabilar Yahuda. (TsA: Mika 5:2; SA: Matiyu 2:1)
6. Mahaifiyar Yesu wata budurwa ce wadda ba ta tapa yin jima ’i da mutum ba. (TsA: Ishaya 7:14; SA: Matiyu 1:18)
7. An kai jariri Yesu xasar Masar don a tsare shi. (TsA: Yusha’ u 11:1; SA: Matiyu 2:14 - 15)
8. Yesu ya tafi yankin Galili don ya koyar da jama ’a. (TsA: Ishaya 9:1 - 2; SA: Matiyu 4:13 - 14)
9. Yesu ne ‘ babban annabi’ wanda Musa ya ambata. (TsA:

Maimaitawar Shari 'a 18:15; SA: Yohanna 6:14)

10. Yesu ne firist namu na har abada. (TsA: Zabura 110:4; SA: Ibraniyawa 6:20)
11. Yesu mai hikima mai ganewa ne. (TsA: Ishaya 11:2; SA: Luka 2:52)
12. Jama 'a rsa ba su karpi Yesu ba. (TsA: Ishaya 53:3; SA:

kurkuku, Bulus ya rubuta cewa, " Markus ... taimake ni xwarai " (Kolosiyawa 4:10- 11).

Markus ya rubuta cewa Yesu Almasihu 'Qan Allah ' ne. Yesu ya ce da kansa 'Qan Mutum. ' Shi ne sunan da Allah ya ba annabawan da ya zapa su faqi saxon Allah ga jama 'a (Ezekiyel 12:2). Amma kuma Allah ya ce Yesu Qansa ne (Markus 1:11 da 9:7). Allah ya zapi wata budurwa sunanta Maryamu, ta zama mahaifiyar Yesu (Luka 1:26 - 35 da 2:1 - 20).

## YI MAGANA A KAN WANNAN:

1. Minene muka sani game da Markus?
2. Ta wace hanya Markus ya koyi labarin Yesu?
3. Yaya Yesu ya bambanta da sauran annabawan Allah?

# ME MARKUS YA CE A KAN YESU?

A wannan sashi na farko na Bisharar Markus, muna karantawa a kan aikin da Yesu ya fara yi lokacin da ya yi shekara 30. Yesu ya zo domin ya yi aikin Allah Ubansa. Ya ciyar da masu yunwa (Markus 8:1 - 13). Ya warkar da marasa lafiya (2:1 - 12). Ya umarci aljanu su fita daga mutane (9:14 - 32). Ya ta da matattu (5:42). Al 'ajaban nan sun nuna mana cewa ya fito daga wurin Allah (ka dubi Yohanna 1:14). Manufar Markus mu san cewa Yesu Qan Allah ne. Yesu ya kawo Bishara, wato Labari Mai Daqi cewa Allah za ya gafarta mana zunubanmu idan mun ba da gaskiya ga Qansa.

Littafi Mai Tsarki ya ce dukan mutane sun yi zunubi (Romawa 3:23). An haife mu cike da zunubi. Saboda haka Allah ya aiko da Qansa ya cece mu. Abu mafi muhimmanci wanda Yesu ya yi dominmu, shi ne ya mutu dominmu. Ya zo ne domin ya sha wuya ya ba da ransa. Daga haihuwarsa ba ya da zunubi. Mu mun cancanci mutuwa domin mu masu zunubi ne. Amma Yesu bai cancanci mutuwa ba. Littafi Mai Tsarki ya koya mana cewa Yesu ya zo don ya mutu dominmu, a madadinmu. Cikin mutuwarsa Yesu ya sha hukuncin zunubanmu. Idan mun gaskanta da Qan Allah, muna da rai na har abada. Tun da daqewa kafin haihuwar Yesu, aka alkawarta abubuwan nan a cikin Rubutacciyar Maganar Allah.

# YARANTAKAR YESU

## * Da farko ka karanta Matiyu sura 1 da 2, kuma Luka sura 1 da 2

Duk da Markus, kuma Matiyu da Luka da Yohanna suka rubuta Bisharu, waqanda suke da labarbarun Labari Mai Daqi game da Yesu Almasihu. Matiyu da Luka sun ba mu labarin haihuwar Yesu da ta Yohanna Maibaftisma (kakansu qaya ne). Markus ba ya ba mu labarun nan a cikin Bishararsa.

Zamanin haihuwar Yesu da Yohanna, sojojin yaxin Roma ne masu mallakar xasar Isra 'ila. Daga birnin Roma, Kaisar Augustas ya ba da umarni ga sojojinsa a Isra' ila cewa su xirga dukan Yahudawa, su rubuta sunayensu (Luka 2:1). Saboda umarnin nan, sai kowane Bayahude ya koma garin da aka haife shi. Augustas ya so sanin jimlar Yahudawa a Isra' ila. Wani mutum mai suna Yusufu yana da alkawarin aure da wata budurwa mai suna Maryamu. Sun tafi Baitalami garin Yusufu tare domin a rubuta sunayensu.

Maryamu tana da ciki. Bai yi kyau budurwa marar aure ta qauki ciki ba. Sa ' anda Yusufu ya ji Maryamu take da ciki, ya yi tunani ya saki Maryamu (Matiyu 1:19). Amma Allah ya yi masa magana a mafarki. Sai Yusufu ya gane cewa cikin nan al 'ajabi daga wurin Allah ne. Ya


auri Maryamu, amma bai kwana da ita ba sai bayan haifuwar Yesu (Matiyu 1:25).

Lokacin da suke a Baitalami sai aka haifi Yesu. Yesu ba qan Yusufu ba ne. Shi Qan Allah ne. Maryamu ta sami ciki ta dalilin ikon Ruhun Allah Mai Tsarki (Matiyu 1:18, 20). Allah ya yi haka domin Qansa ya kasance marar zunubi tun daga haihuwarsa.

Bishara ta hannun Luka ta ba mu labarin haihuwar Yohanna Maibaftisma. An haife shi wata shidda kafin haihuwar Yesu (Luka 1:5 - 24 da 57 - 66). Haihuwarsa kuma al 'ajabi daga wurin Allah ne (Luka 1:7 da 13). Amma shi ba qan Allah ba ne. Shi qan Zakariya ne. Markus ya ba mu labarin shirin Allah don Yohanna. (Za mu yi nazarin wannan nan gaba.)

An faqa ma makiyaya inda za su sami jariri Yesu, su yi masa sujada (Luka 2:12). Mala' iku daga wurin Allah sun shaida masu labarin nan mai ban mamaki. Allah ya so talakawa su san labarin haihuwar Qansa.

A zamanin nan, Augustas ya naqa Hirudus sarki bisa Isra 'ila. Hirudus sarki mugu ne xwarai, mai zalunci. Wata rana manya daga gabas sun iso fadar Hirudus. Mukan kira su ‘ Shehuna ukku.’ Sun zo Isra 'ila neman sabon jariri Sarkin Yahudawa. Sun bi sabon



tauraro (Matiyu 2:2). Amma Yesu ba ya nan fadar sarki. Ina yake? Hirudus ya tambayi shugabannin addini. Sun karanta abin da annabi Mika ya ce cikin Rubutacciyar Maganar Allah, cewa za a haifi Almasihu a Baitalami (Mika 5:2). Shi ne inda shehuna sun sami jariri Yesu. Sai masu hikima su karanta Littafinsu Mai Tsarki. Sa' an nan za su san hanyar da ya kamata. Hirudus bai so wani Bayahude ya zama sarki a madadinsa ba. Shi ya sa ya kashe dukan jarirai a wajen Baitalami (Matiyu 2:16). Abin tausayi, labarin da mugun sarki ya ji daga shehuna ya tura shi ga yin wannan.

Maryamu da Yusufu sun tsira, sun yi gudu zuwa Masar tare da Yesu (Matiyu 2:13). Mala' ikan Allah ya shaida masu abin da za su yi, kuma daga baya ya bishe su gida a Nazarat (Matiyu 2:22 - 23). Yesu ya zauna a garin nan kusan shekara 30. Mutane sun qauke shi qan Yusufu ne wanda ke kafinta a Nazarat.

Yesu ya yi ta xaruwa da hikima da tsayi (Luka 2:52). Amma mutane da yawa ba su gaskanta ba cewa shi Qan Allah ne. Dab da lokacin mutuwarsa Yesu ya faqa ma Bilatus cewa, 'Wannan shi ne dalilin da aka haife ni, shi ne kuma dalilin da na shigo duniya, don in shaida gaskiya' (Yohanna 18:37). Mala' iku sun ce Yesu ya zo ya zama Mai Ceto, Almasihun da aka alkawarta (Luka 2:11). Simiyon ya ce Yesu ya zo domin ya kawo haske wurin al ' ummai da qaukaka ga Yahudawa (Luka 2:32). Annabiya Hannatu ta ce Yesu ne Mai Ceto (Mai Fansa)

## Sunayen da Markus ya ba Yesu

| | |
|---|---|
| Yesu Almasihu (1:1) | Ubangiji na Ranar Hutu (2:28) |
| Qan Allah (1:1 da 3:11) | Qan Allah Maqaukaki (5:7) |
| Yesu Banazare (1:24) | Kafinta (6:3) |
| Mai Tsarkin nan na Allah (1:24) | Qan Maryamu (6:3) |
| Ubangiji (1:3 da 7:28) | Almasihu (8:29) |

wanda kowa a Urushlima ke jira (Luka 2:38). Me ka gaskanta game da dalilin da Allah ya aiko Yesu zuwa cikin duniya?

### YI MAGANA A KAN WANNAN:

1. Mala 'i kan Allah ya yi magana da uban Yohanna (Luka 1:13 - 20), da kuma uwar Yesu (Luka 1:26 - 38), da kuma Yusufu (Matiyu 1:20 - 25). Yaya suka aikata zancen abin da aka faqa masu? Me muke koyo daga wannan?
2. Ta wace hanya shehuna daga gabas suka sami bishewa game da Sarki Yesu? Ta yaya makiyaya suka sami labarin Yesu? Ta wace hanya ya kamata mu nemi bishewar Allah a rayukanmu?
3. Minene abin da waqannan mutane suka gaskanta a kan

haihuwar Yesu: Maryamu, sarki Hirudus, shehunan gabas, makiyayan Baitalami, Simiyon da Hannatu a Urushalima? Me ka gaskanta game da haihuwar Yesu? Wanene Yesu? Daga ina yake? Me zai kasance nan gaba?

* Yanzu ka karanta Markus 1:1 -13 *(Labarun nan kuma suna cikin Matiyu 3:1 -17 da 4:1 - 11; Yohanna 1:19- 34)*

## YOHANNA MAIBAFTISMA

### YA SHIRYA HANYA DOMIN YESU

A cikin ayoyin nan 13 muna saduwa da dukan manyan mutanen Bishara ta hannun Markus:

a) Yohanna Maibaftisma, wanda ya yi wa' azi cikin daji (1:4)

b) Yesu Qan Allah, wanda ya zo daga Sama (1:9)

c) Allah Ruhu Mai Tsarki, wanda ya sauko bisa Yesu

**Majami' ar Yahudawa**


Ga abin da ake yi a majami ' ar Yahudawa:

1. Ana yi ma Allah sujada da addu 'a.
2. Kowace rana ana karatun Rubutattun Littattafai na Yahudawa (wato, Tsohon Alkawari), ana kuma koyar da su.
3. Akwai makaranta domin yara maza.

(1:10)

d) Allah Uba, wanda ya yi magana daga Sama (1:11)

e) Shaiqan, wanda ya gwada Yesu (1:13)



f) Mala 'i ku, waqanda suka yi ma Yesu hidima (1:13)

Yohanna Maibaftisma yana da kamannin annabin Allah. Rayuwarsa da maganarsa sun zama na manzo daga wurin Allah (1:6). Ya zama daidai kamar yadda annabi Malakai da annabi Ishaya suka kwatanta shekara 700 kafin haifuwarsa. Sun yi zancen muryar manzo da ke kira, "Ka shirya hanya a jeji domin Ubangiji!" (Ishaya 40:3; Malakai 3:1). Markus ya mori maganar annabawan nan domin ya shaida mana kowanene Yohanna (Markus 1:2 - 3).

Har ma kafin haihuwarsa, Allah ya cika Yohanna da Ruhunsa domin ya yi aikin nan (Luka 1:13 - 14). Yohanna ya zo ne domin ya gargaqa ma mutane cewa su bar yin mugunta, su tuba, a yi masu baftisma (Markus 1:4).

Sa 'anda mutane suka tuba daga mugayen ayyukansu, sai Yohanna ya yi masu baftisma. Wato, ya sa su shiga xarxashin ruwa, sa 'an nan ya ta da su. Wannan ya zama misali ga duniya cewa sun tuba. Ma' anar ' tuba ' ke nan, muna baxin ciki saboda zunubanmu,

muna son barinsu, mu juya masu baya, mu koma ga bin hanyar Allah. Zunubanmu sun xumshi kowane mugun abin da muka faqa, da kowane laifin da muka yi, da kowane mugun tunaninmu, har ma abubuwa masu kyau waqanda ya kamata mun yi amma ba mu yi su ba. Zunubi ya raba mu da Allah, domin Allah mai tsarki, nagari cikakke, marar zunubi ne. Shiga xarxashin ruwa alama cewa Allah ya wanke tsohuwar rayuwarmu, mu zama sababbi domin mu fara sabon rai tare da Shi.

Allah ya yi alkawari cewa zai ceci jama 'ar Isra 'ila daga maxiyansu, kuma ya sake zuba masu albarku. Allah ya yi alkawarin Mai Ceto. Annabawa da yawa a Tsohon Alkawari sun yi magana a kan wannan. Amma ya yi shekara 400 ba a sami annabi na musamman ba. Mutane da yawa sun fid da zuciya. Sa 'an nan Yohanna ya zo! Ya zo domin ya shirya ma Yesu hanya, shi wanda ke Almasihu ne. Yohanna ya faqa ma jama' a zancen Yesu B wato, ya ce wani mai muhimmanci yana zuwa (1:7- 8). Bayan wannan Ruhun Allah ya tura Yesu cikin daji don Shaiqan ya gwada shi (dubi Matiyu 4:3 - 9).

## YI MAGANA A KAN WANNAN:

1. Ta wace hanya mutane suka sani Yohanna annabi ne (1:6)?
2. Me Yohanna ya zo ya yi?
3. Me Yohanna ya faqa a kan Yesu (1:7)?
4. Me Yohanna ya tambayi mutane kafin ya yi masu baftisma

(1:4)?

5. Mecece ma 'anar tuba?
6. Ta wurin samun baftisma, Kirista suna sa abokansu su yi tunani a kan Allah da Yesu da Labarinsa Mai Daqi: Wannan zance gaskiya ne ko kuwa xarya?

## YOHANNA YA YI MA YESU BAFTISMA

Yesu ya zo daga Galili zuwa Kogin Urdun, Yohanna ya yi masa baftisma (Matiyu 3:13). Babu wani dalilin da Yesu zai tuba, domin ba ya da zunubi (Ibraniyawa 4:15). Yohanna ya yi ma Yesu baftisma domin ya yi kyau haka (Matiyu 3:15). Shirin Allah ne, ya yi daidai domin ya zama misali ga mutane. Yohanna ya zo domin ya shirya hanya domin aikin Yesu. Shi ne shirin Allah domin Yohanna.

Lokacin da Yesu ya fito daga ruwa, Yohanna ya ga manyan alamu ukku:

a) Sama ta 'buqe'.
b) Ruhu Mai Tsarki ya sauko bisa Yesu.
c) Wata murya daga Sama ta ce, Wannan shi ne Qana da nake xauna, wanda nake jin daqinsa xwarai."

An jima Yohanna ya ce, “ Na ga Ruhu yana saukowa da kamannin kurciya daga sama, ya kuma zauna a kansa. A dâ ni ma ban san shi ba, sai dai Allah wanda ya aiko ni in yi baftisma da ruwa, shi ne ya ce mini, ‘ Mutumin da ka ga Ruhu yana sauko masa ya kuma zauna a kansa, to, shi ne mai yin baftisma da Ruhu Mai Tsarki. ’ Na kuwa ga haka ya faru, na kuma shaida cewa, wannan mutum Qan Allah ne. ” (Yohanna 1:32 - 34)

### YI MAGANA A KAN WANNAN:

1. Ko Yohanna ya san kowanene Yesu (Yohanna 1:32 - 34)?
2. Me ya sa Yesu ya roxi Yohanna ya yi masa baftisma cikin kogin?
3. Me Allah Uba ya ce game da Qansa Yesu?
4. Waqanne annabawa suka yi magana a kan Almasihu (Maimaitawar Shari ’a 18:18, Ishaya 7:14)?

* **Yanzu ka karanta Markus 1:14 –20 (Labarun nan kuma suna cikin Matiyu 4:12 - 22; Luka 4:14 –15 da 5:2 – 11)**

## LABARI MAI DAQI A KAN YESU ALMASIHU

Yohanna Maibaftisma ya kira mutane ga tuba su ba da gaskiya ga Yesu wanda ke Almasihu. Muna tuba idan muna jin baxin ciki

saboda zunubanmu, muna juya masu bayanmu. Yohanna ya faqa ma Sarki Hirudus cewa laifi ne ya auri matar qan ' uwansa. Saboda haka Hirudus ya qaure Yohanna a kurkuku. Daga baya ya kashe Yohanna.

Shaiqan ba ya iya kome banda sanin Allah. Ba abin da ke faruwa da mu sai an xaddara. Allah mai sani duka ne, mai iko duka kuma. Shirye - shiryen Allah ba su tapa faquwa, abin da ya nufa za ya tabbata (Ishaya 46:9 - 10).

Shekara da shekaru Yahudawa sun yi begen Almasihu. Sun sa ido ga shugaba wanda zai cece su daga hannun Romawa magabtansu. Amma da farko Allah ya so su koma wurinsa, su juya bayansu ga miyagun hanyoyinsu. An kashe mutanen Allah masu kirki da yawa waqanda suka yi xoxarinsu su ceci Yahudawa daga mummunan tafarkinsu da kuma munanan hanyoyin al ' ummai. Annabawa Yahudawa sun ba da labarin Wani mai zuwa wanda zai cece su. Mutumen nan Mai Ceto (Almasihu) zai zo ya ceci dukan al ' ummai, da Yahudawa da waqanda ba Yahudawa ba ne. Mutumen nan zai maido mana dukan abubuwan da suka pace lokacin da Adamu ya aikata zunubi na farko (Farawa 3:17 - 19; Maimaitawar Shari ' a 18:15; Ishaya 42:1; 49:6; Galatiyawa 3:16). Mutumen nan Yesu ne. Yesu ya faqa masu cewa mulkin Allah ya yi kusa. Mulkin zai kasance wuri a zukatan jama ' a inda Shi yana cetonsu yana mulkinsu.

YI MAGANA A KAN WANNAN:

1. Minene Labari Mai Daqi wanda Yesu ya faqa ma jama 'a

> **Ranar Assabaci**
>
> Ma 'anar "Assabaci" ita ce hutawa, wato barin yin aiki. Allah ya gaya wa Adamu yadda ya halicci sama da xasa cikin kwana shidda na aiki. A rana ta bakwai Allah ya ce ya huta daga aikinsa. Ya kira kwana na bakwai Assabaci ko Asabar (Farawa 2:3). Daga baya Allah ya ba Musa dokokinsa. Cikin Dokar Allah, ranar Asabar rana mai tsarki ce (Fitowa 20:8 -11). A ran Assabaci mutane maza da mata sun huta daga aikinsu domin su yi ma Mahaliccinsu sujada. Ranar Assabaci ta zama ranar xarshen mako, wato rana ta bakwai. Ta fara da faquwar rana ran Jumma' a. Abin baxin ciki ne, Farisiyawa sun xara dokoki na kansu game da ran nan. Sun mai da hankali ga xa 'i dodinsu na ranar Asabar fiye da yi

(Markus 1:14 -15; Yohanna 17:3)?

2. Me Shaiqan ya yi da nufi ya pata shirin Allah?
3. Me ya sa dole mutane su tuba (1:15)?
4. Har yanzu — mecece ma' anar tuba?

# YESU YA KIRA MA' AIKATA SU BI SHI

Yesu yana yawo a bakin Tekun Galili. Ya ga van ' uwa biyu, wato Siman da Andarawus. Suna jefa raga cikin ruwa don su kama kifi (1:16). Yesu ya kira su, ya ce, "Ku biyo ni!" Ya so ya koya masu game da mulkin Allah. Ka lura, Yesu ya kira ma ' aikata talakawa su bi shi.

Nan da nan sun bar kamun kifi, suka bi Yesu. Ya yi masu alkawari cewa, "Zan mai da ku masu jawo mutane zuwa wurina" (1:17).

Andarawus qaya daga almajiran Yohanna ne. Ya bar Yohanna, ya bi Yesu. Sa' an nan Andarawus ya koma wurin qan 'uwansa ya ce masa, "Ai, mun sami Almasihun" (Yohanna 1:40- 41).

Sa 'an nan Siman ya ba da gaskiya ga Yesu Almasihu, ya zama almajirin Yesu. Daga baya Yesu ya faqa ma Siman cewa, "Za a ce da kai Kefas." A helenanci suna Kefas da Bitrus duk qaya ne, ma ' anarsu 'dutse' ce (Yohanna 1:42). Wannan Bitrus shi ne mutumen da ya koya ma Markus dukan abin da ya sani game da Yesu.

Yanzu Yesu a shirye yake ya ba almajiransa koyarwa, kuma ya shaida ma jama ' a labarin mulkin Allah da tsarkinsa.

## * Yanzu ka karanta Markus 1:21 - 28

*(Labarin nan kuma yana cikin Luka 4:31 - 37)*

# YESU YA FARA WA'AZI DA WARKASWA

Yesu ya shiga majami'a a Kafarnahum, wuri inda Yahudawa ke sujada. A wurin ya koyar da jama'a (1:21). Sun yi mamakin koyarwarsa. Shugabanninsu sukan karanta masu Shari'ar Allah kowace ran Asabar, amma Yesu ya yi magana a kan mulkin Allah da hakikancewa (1:22). Maganarsa tana da iko xwarai. Ya ce mulkin Allah ya yi kusa, sai su shiga albarkunsa.

Maganar Yesu da iko xwarai, har ta sa wani mutum ya ta da ihu cewa, "Ina ruwanka da mu, Yesu Banazare? Ko ka zo ne ka halaka mu? Na san wane ne kai, kai ne Mai Tsarkin nan na Allah!" (1:24). Wani mugun aljani a cikinsa ya sa yana tsoro ya yi maganan nan. Yesu ya gane ba mutumin da ke magana ba, amma aljanin da ke cikinsa. Yesu ya umarci aljani, ya ce, "Ka yi shiru! Ka fita daga cikin mutumin nan!" Sai xazamin aljani ya bugi mutumin ya fita. Mutane sun yi mamaki sosai. Sun ce, " Wannan mutum yana da iko yâ ba aljanu umarni, suna kuwa yi masa biyayya!" (1:27).

Ka lura, Yesu "Bai ko yarda aljanun su yi magana ba, domin sun san shi" (1:25, 34). Yesu bai yarda Shaiqan sarkin aljanu ya faqi sunansa ba. Amma ba da daqewa ba, kowa ya ji zancen koyarwar Yesu, da kuma dole baxaxen aljanu suna yi masa biyayya. (1:27-28).

## YI MAGANA A KAN WANNAN:

1. Ko gaskiya ce, ko kuwa xarya ce, Yesu yake son masu ilimi kaqai su zama almajiransa?
2. Me ya sa mutane sun yi mamakin koyarwar Yesu?
3. Yaya mugayen aljanu sun san Yesu?

### * Yanzu ka karanta Markus 1:29 - 45

*(Labarun nan kuma suna cikin Luka 4:38 - 44)*

## BITRUS YA KAI YESU GIDA

A bakin Tekun Galili ga arewa akwai wani gari sunansa Kafarnahum. Yesu ya yi ziyara a gidan Siman Bitrus. Surukar Bitrus ba ta da lafiya. Yesu ya tafi wurinta, ya kama hannunta, ya qaga ta. Nan da nan zazzapi ya bar ta, sai ta yi masu hidima. (1:31). Yesu yana da ikon Allah domin ya aikata al 'ajabai. Ya warkar da marasa lafiya.

Da faquwar rana sai mutanen gari sun matso ma xofa (1:33). Sun kawo marasa lafiya da masu aljanu wurin Yesu. Ya warkar da su duka.

Gari ya waye sai Siman Bitrus ya kira sauransu, sai suka fita neman Yesu. Yakan tashi da sauran duhun dare, ya tafi inda ba kowa domin ya yi addu' a (1:35). Yana magana da Ubansa cikin Sama. Ta hanyar yin addu 'a, sai kullum yana tafiya bisa ga nufin Allah Ubansa, kuma tare da ikonsa.

Bitrus ya sami Yesu, ya ce masa, “ Ai, dukan mutane suna nemanka! ” Yesu ya amsa ya ce, “ Mu je garuruwan da suke gaba. ” Sai suka zazzaga dukan wannan yankin Galili. Yesu ya yi wa ’ azi a

MISALAI


- Yesu ya mori misalai domin ya koya ma masu binsa gaskiya. Misali wani labari mai sauxin ji a kan abubuwan da ke faruwa yau da gobe, amma kuma yana da wata ma ’ana mai zurfi ta ruhaniya.
- Sau da dama daga baya Yesu ya bayanna ma almajirai goma sha biyu ma ’anar misalin (4:13).

majami’ unsu. Kuma ya fitar wa mutane baxaxen aljanu (1:39).

## YESU YA WARKAR DA KUTURU

Wani kuturu ya zo wurin Yesu. Yahudawa suna kiran ciwon fatar jiki iri -iri da suna kuturta. Mutumen ya durxusa, ya roxi Yesu ya taimake shi. Doka ta sa kutare suke zaune nesa da garuruwa da xauyuka. Ya ce, “ Idan ka yarda, kana iya ka tsarkake ni. ” Yesu ya ji tausayinsa sosai. Ya mixa hannu, ya tapa shi. Ya ce, “ Na yarda,

ka warke! ” Nan da nan mutumen ya sami lafiya. Sai Yesu ya ce, “ Ka je ka nuna kanka a wurin firist. ” Ya zama dole mutumen ya yi haka domin ya sami shaida cewa ya warke.



Bayan wannan, za a yarda ya koma gida wurin iyalinsa. Yanzu babu sauran zaman kaqaici, da bukatar yin kira, “Marar tsarki, marar tsarki! ”

Yesu ya sake yin niyya ya hana mutumen shi gaya ma kowa (1:44). Amma sai mutumen ya baza labarin ko ’ ina. Shi ya sa ya yi wuya Yesu ya tafi waqansu garuruwa saboda taron mutane (1:45).

## YI MAGANA A KAN WANNAN:

1. Lokacin da Yesu ya warkar da kuturu, me ya sa ya ce “Kada ka gaya wa kowa ”?
2. Don me dole mutumen da aka warkar da shi ya nuna kansa a wurin firist?
3. Ka nemi sauran wurare a Markus inda Yesu ya yi addu ’a da sassafe.
4. Me Yesu ya ce ma Siman Bitrus (Yohanna 1:42)?
5. Ta yaya almajirai za su kama mutane?

## * Yanzu ka karanta Markus 2:1 -12

*(Labarin nan kuma yana cikin Luka 5:18 -26)*

# YESU YA WARKAR DA SHANYAYYE


Yesu ya koma gidan Siman Bitrus. Mutane da yawa sun ji labarin zuwansa, sun taru sai sun cika gidan har babu sauran wuri (2:2). Yesu ya yi masu wa 'azin maganar Allah. Maganar Allah ita ce Labari Mai Daqi (wato Bishara) a kan xaunar Allah wadda muke gani cikin Yesu (Ayyukan Manzanni 8:4).

A xasar Isra 'ila, ana yin gidaje da manyan duwatsu. Yawansu soraye ne masu yepen laka waqanda ake kwana a bisa. Waqansu qakuna suna da rufin katako da fale -falen birgi.

Mutum huqu sun kawo wani abokinsu wanda bai iya tafiya ba. Sun zo gidan inda Yesu yake wa 'azi. Sun kasa shiga. Saboda haka sun hau bisa soro, sun buqe rufin gida. Sa 'an nan sun saukar da abokinsu marar lafiya duk da tabarmarsa daidai inda Yesu yake. Kullum bangaskiya ga Allah takan sa mutane su yi aikin jaruntaka. Masu bangaskiya suna yin manyan ayyukan domin suna dogara ma Allah mai girma. Yesu ya ga bangaskiyarsu. Sai ya ce ma shanyayye, "Qana, an yafe maka zunubanka." (Ka lura, magana "Qana" a nan ta zama gaisuwar kirki, Yesu ba mahaifinsa ba ne.)

Waqansu Farisiyawa da malaman Dokar Musa sun ji maganar Yesu. Farisiyawa malamai Yahudawa waqanda sukan xara dokokin addini da yawa, su haqa da dokokin Allah. Sun yi gunaguni cewa, “Wa yake da ikon yafewar zunubi in ba Allah kaqai ba?” (2:7). Sun ce Yesu yana yin sapo, wato yana magana gâba da Allah (Zabura 74:18; Ishaya 52:5; Romawa 2:24). A zamanin Tsohon Alkawari, shugabanni Yahudawa sukan yanke wa masu yin sapo hukuncin kisa a jefe su; Littafin Firistoci 24:11 -14).

Yesu ya gane tunaninsu. Ya tambaye su, “Wanne ya fi sauxi, a ce wa mai ciwon nan, ‘An yafe maka zunubanka,’ ko kuwa a ce, ‘Tashi ka qauki tabarmarka ka yi tafiya’?” Ya faqa haka domin ya gwada masu shi Qan Allah ne, yana da iko bisa duniya ya yafe zunubai ya warkar da mutane (2:9 -10). Sa'an nan ya warkar da mutumen.




Kowa ya ga mutumen ya tashi ya tafi gida. Sai sun qaukaka Allah cewa, “ Ba mu tapa ganin wani abu kamar haka ba” (2:12).

## * Yanzu ka karanta Markus 2:13 –17

*(Labarin nan kuma yana cikin Luka 5:27 –32)*

# YESU ABOKIN MASU ZUNUBI

Sa 'an nan Yesu ya fita ya yi magana da taro a bakin teku. Yana son mutane su bar dukan kome su bi shi. Ran nan ya sami Lawi, wani mai karpar haraji wanda sunansa kuma Matiyu ne. Masu karpar haraji suna aiki domin mulkin Roma. Saboda haka mutane ba su son su ba, kuma domin su marasa gaskiya ne. Suna karpar haraji wurin Yahudawa, kuma sukan xwara kuqi da yawa. Yahudawa suna kiransu masu zunubi. Lawi ya bar aikinsa, ya bi Yesu (2:14).



Lawi ya gayyaci Yesu da almajirai su ci abinci a gidansa. Waqansu Yahudawa malaman dokoki waqanda su Farisiyawa ne suna wurin. Sun yi tambaya cewa, " Me ya sa (Yesu) yake ci tare da masu karpar haraji da masu zunubi? " Yesu ya amsa ya ce, "Masu lafiya ba sa bukatar likita, sai dai marasa lafiya. Ban zo don in kira masu adalci ba, sai dai masu zunubi " (2:17). Yesu yana so ya taimaki waqanda suke da bukatar xwarai. Waqannan suka karpi Yesu da kyau, amma shugabannin addini ba su so su bi Yesu ba. Shugabanni da sauran jama 'a suna neman Almasihun da aka alkawarta, amma ba su son Yesu.

## YI MAGANA A KAN WANNAN:

1. Ko gaskiya ce, Yesu kaqai yake da iko ya gafarta zunubai kamar yadda Allah ke iyawa?
2. Me ya sa Yesu ya ce, “ Masu lafiya ba sa bukatar likita ”?
3. Don me shugabannin Yahudawa ba su ji daqi ba lokacin da Yesu ya ci abinci tare da masu muguwar tarbiyya?
4. Me ya sa marasa kyau suka zo wurin Yesu?

## * Yanzu ka karanta Markus 2:18 - 22

*(Labarin nan kuma yana cikin Luka 5:33 - 38)*

## YESU YA NUNA HANYA MAFI KYAU

Farisiyawa sun qauki kansu cewa su kaqai ne nagargaru. Suna azumi, wato ba sukan ci abinci a waqansu ranaku ba. Suna xoxari su yi biyayya ga dukan dokokin Allah.



Allah ya ce dukan mutane masu zunubi ne. “Ba wanda ke aikata abin da ke daidai, babu ko qaya ” (Zabura 53:3. Dubi kuma Romawa 3:10 da 23).

Almajiran Yohanna suna yin azumi.

Mutane sukan yi azumi domin waqansu dalilai:

a) Su bayyana baxin ciki a lokacin mutuwa (Zabura 35:13)

b) Su ba Allah hankalinsu, su yi masa sujada (Nehemiya 1:4)
c) Su kiyayi doka a kan ranaku na musamman, misali Ranar Kafara
d) Su xara ba da kansu ga yin addu' a saboda wani babban dalili ko matsala

Yesu ya yi misali da bikin aure na Yahudawa. Al ' adar Yahudawa, gidan ango da gidan amarya a buqe suke domin baxi su shiga. Sai baxi su ji daqin biki, su yi murna tare da ango da amarya. Yesu ya ce haka yake duk lokacin da yake tare da su, domin shi Ango ne. Zai kasance tare da su qan xaramin lokaci kaqai, sai su yi farin ciki. Sa ' an nan za a kashe shi, sai za su yi baxin ciki. A lokacin nan zai cancanta su yi azumi (2:20). Yesu ya zo don ya nuna masu hanya mafi kyau. Amma a haqa tsoffin al 'adu da sabuwar koyarwa ba zai yi ba (2:21 - 22). Yesu yana son mutane su bar tsohuwar hanyarsu, su bi shi.

## * Yanzu ka karanta Markus 2:23 - 28; 3:1 - 6

*(Labarun nan kuma suna cikin Luka 6:1 - 11)*

## YESU YA WARKAR DA MUTUM A RANAR ASABAR

Farisiyawa suna jin haushi. Yesu ya san cewa suna neman hanya su kashe shi (3:6). Suna gardama da Yesu a kan abubuwan da suka hana a ranar Asabar, wato Ranar Hutu ko Ranar Ubangiji.

## ALMAJIRAN YESU GOMA SHA BIYU (Markus 3:13 - 19)

**Siman** daga Betsaida. Mai kamun kifi ne. Yesu ya sa masa suna **Bitrus** (wato, dutse).

**Yakubu** qan Zabadi, wanda ake kira '**Yakubu babba**'.

**Yohanna**, qan 'uwan Yakubu.

**Andarawus**, qan ' uwan Bitrus (Yohanna 1:40).

**Filibus**, wanda ya tafi neman

**Nataniyel**, wanda ake kira **Batilomi** (Yohanna 1:43).

**Yakubu** qan Halfa, wato '**Yakubu xarami**' (Markus 15:40).

**Matiyu** mai karpan haraji, sunansa kuma **Lawi** (Matiyu 10:2).

**Taddiyus**, wanda ake kira **Yahuza.**

**Siman** mai kishin xasarsu (Luka 6:15).

**Yahuda Iskariyoti**, mutumin Kariyot wanda daga baya ya ba da Yesu).

Suna nemen dalili cikin maganganunsa domin su kai xararsa.

Yesu ya warkar da mai shanyayyen hannu. Sai hannunsa ya sami lafiya da xarfi yadda ya kamata. Ya warkar da shi a ranar Asabar. Yesu ya san tunanin Farisiyawa. Sai ya tambaye su a kan abin da Doka ta aminta a yi, "Mene ne ya dace a yi a Ranar Hutu? A yi alheri ko a yi mugunta?" (3:4).

Kafin wannan, almajirai sun karya waqansu kan hatsi suna ci. Sai Farisiyawa sun ce dokar Ranar Asabar ta hana (2:23 - 24). Yesu yana

fushi da Farisiyawa, amma kuma yana jin tausayinsu saboda taurin zuciyarsu (3:5). Farisiyawa ba su amsa kome ba, amma sun fita don su shirya yadda za su kashe shi (3:6). Yesu ya nuna ma mai ciwon hannu alheri, amma yana tausayin shugabannin addini saboda taurin zuciyarsu.

Ka lura da 2:28. Wurin da Yesu yana magana a kan Qan Mutum, yana nufin shi kansa. Yesu Ubangijin dukan kome ne.

* Yanzu ka karanta Markus 3:7 - 19

## YESU YA ZAPI MUTUM GOMA SHA BIYU

Yesu ya shiga wani gida wajen teku. Mutane da yawa sun zo daga garuruwa kusa da nesa don su saurare shi. Taro sun matsa ma Yesu xwarai, da kyar ya ci gaba da maganarsa. Sai ya shiga jirgin ruwa ya koya masu daga can. Daga baya ya tafi ya hau dutse.

Da sassafe ya kira masu binsa, ya zapi mutum goma sha biyu su zama almajiransa na musamman. Domin:

a) su kasance tare da Yesu

b) ya koya masu


c) ya aiko su wurin yin wa ' azi

d) ya ba su ikonsa na yin warkaswa da kuma fid da aljanu (3:15)

Domin shekara ukku Yesu ya koyar da almajirai goma sha biyu,

wato manzanni, yadda za su zama masu kawo saxon Allah.

YI MAGANA A KAN WANNAN:



1. Ko laifi ne a karya hatsi a ranar Assabaci?
2. Me ya sa mutane suka yi azumi?
3. Minene abubuwan da suka cancanta mu yi a ranar Assabaci?
4. Minene nufin Yesu da ya ce, "An yi Ranar Hutu domin mutum ne" (2:27)?
5. Minene bambanci tsakanin koyarwar Yesu da koyarwar shugabannin addini?
6. Yaya mutane za su koya su zama masu kawo saxon Allah?

## * Yanzu ka karanta Markus 3:20 - 30

(Labarin nan kuma yana cikin Luka 11:14 - 23)

# KOYARWAR YESU A KAN IKON ALLAH BISA SHAIQAN

Yesu ya fitar da aljanu daga mutane (1:39). Farisiyawa sun yi magana a kai. Sun ce da ikon sarkin aljanu Yesu yake fitar da aljanu (3:22).

Yesu ya tambaye su, “Shaiqan zai fitar da Shaiqan kuma?” Maganar wauta ce. Yesu ya ba da misalai ukku domin ya bayyana wannan:

a) mulki inda mutane suke faqa da juna

b) gida ko iyali inda mutane suke faqa

c) Shaiqan yake faqa da kansa

Akwai mulkin ruhu biyu a duniyan nan: Mulkin Allah wanda ke mulkin haske da xauna, da mulkin Shaiqan wanda ke mulkin duhu da mugunta. Aljanun Shaiqan suna xin gaskiya, suna yaxi da bayin Allah. Shi ya sa Yesu ya koya ma masu binsa yin addu'a cewa, “Ka tsare mu daga Mugun nan” (Matiyu 6:13).

Amma cikin Mulkin Allah ana cin nasara da mugunta, ana kuma gafarar zunubai (3:28). Amma babu gafara ga mai faqin maganar reni, wato sapo gâba da Allah Ruhu Mai Tsarki (3:29).

Shaiqan ne Amutum mai xarfi” cikin misalin Yesu (3:27). Yakan qaure mutane cikin zunubansu. Yesu ya zo ya mutu domin ya qaure mutum mai xarfi, ya saki qaurarrunsa. Yesu ya zo ya vantar da mu daga zunubanmu (Galatiyawa 3:22). Kuma ya zo ya vantar da mutane daga dokokin hannun mutum na Farisiyawa (Galatiyawa 3:23).

### * Yanzu ka karanta Markus 3:31 - 35

## YESU DA UWARSA DA |AN'UWANSA

Da fari idan mun karanta nassin nan, sai mu qauka cewa Yesu ba ya son ganin mahaifiyarsa da van' uwansa. Amma wata aya ta nuna a sarari cewa sun zo don su tafi da shi (3:21). Sun damu a kan abubuwan da mutane suke faqi can gida a Nazarat. Abokansu da maxwabtansu suna cewa Yesu ya haukace.

Saboda haka Yesu bai tashi ya ga iyalinsa ba don kada su tauye nufin Allah. Ya nuna masu jinxai domin ba ya so su yi wani abu gâba da nufin Allah. Maimakon ya tashi, Yesu ya zauna tare da masu yin nufin Allah, wato mutanen da ke son koyarwa da warkarwa. Ya ce sun zama kamar tsohuwa da van 'uwa a gare shi. "Duk wanda ya yi abin da Allah yake so, shi ne qan 'uwana, ita ce var 'uwata, ita ce kuma mamata" (3:35).

Littafi bai fita a fili ya ce Yesu ya xi ganin tsohuwarsa da van' uwansa ba. Amma da ya fita waje ya gan su, da zai zama dole ya gargaqar da su cewa suna yi ma nufin Allah rashin biyayya ta wurin xoxarin kiransa waje. Shi ya sa muna qaukar cewa ya tsaya inda yake. Ya zapa ya zauna tare da masu yin nufin Allah. Gaskiya, ta wurin yin haka ya yi abin da ke daidai da kuma mai alheri game da iyalinsa.

Wani lokaci, mutanen gidanmu mafi kusa gare mu suna ba mu wuya cikin yin nufin Allah. Yakan zama ta dalilin xaunarsu dominmu da suke aikatawa haka. Amma sai mu dogara ga Allah ya taimake mu cikin kowane hali, duk da na cikin gida lokacin da dole mu tsai da magana.

YI MAGANA A KAN WANNAN:

1. Ta wace hanya Yesu ya bayanna xaunarsa domin tsohuwarsa da gidansa?
2. Wanene da farko ya kamata mu yi tunani a kansa lokacin yanke shawara a gida?
3. Masu bin Yesu su ne sashin wani iyali da ke ko'ina a duniya (Markus 3:34 -35). Me wannan ya nuna ma mutanen duniya?

## TAMBAYOYI A KAN MARKUS 1 – 3

(Amsoshi suna a kan shafi 42)

**A. Ka zapi amsa mafi kyau daga waqanda aka ba da.**

1. Tun da daqewa annabawa sun rubuta labarin wani wanda zai kawo saxo daga Allah. Wanene shi?

   a) Yesu
   b) Yohanna Maibaftisma
   c) Bitrus

2. Wa ya ce, "Kai ne Qana wanda nake xauna"?

   a) Allah ga Yesu
   b) Yohanna ga Yesu
   c) Yesu ga Yohanna

3. Ta wace hanya Yesu ya koyar da jama'a?

a) Daidai yadda marubuta suke yi

b) Ya yi amfani da labarun yara

c) Ya mori labaru waqanda suke da wata ma' ana a poye

4. Me ya sa mutum huqu suka huda rufin gida?

a) Don su saukar da mai ciwo a gaban Yesu

b) Don su yi kallon taro

c) Don su lexa asirin Yesu

5. Don me Yesu ya ci abinci tare da masu karpar haraji da masu zunubi?

a) Don ya ba Farisiyawa haushi

b) Don yana jin yunwa

c) Yana so ya nuna masu yadda Allah yake sonsu

6. Saboda me Farisiyawa suke kallon Yesu?


a) Don su koyi yadda za a warkar da mutane

b) Don su sami Yesu da laifi

c) Domin Yesu malami ne na xwarai

7. Waqanne irin mutane

Tafiye tafiyen Yesu



## WARKAR DA MARASA LAFIYA

Yakubu ya rubuta, "Akwai mai rashin lafiya a cikinku? Addu'ar da aka yi cikin bangaskiya za ta warkar da marar lafiya" (Yakubu 5:14 -15). Marar lafiya ta xumshi rashin lafiya ta jiki ko ta ruhu. Zunubi ya iya sa rashin lafiya. Damuwa, da yawan aiki, da ciwo duka sun iya sa rashin lafiya. Waqansu sun tapo a hankalinsu. Waqansu suna da rashin lafiya saboda aljannu. Allah yana da iko ya warkar da dukan irin ciwuce-ciwuce. Ya kamata marar lafiya ya san bukatarsa, wato ya gane bukatar taimakon Allah. Sai su kira dattipan ikilisiyar wuri inda suke da zama. A cikin al'ummar Kirista su ne shugabanni masu ruhaniya. Suna da shugabanci saboda su masu bangaskiya ne. Sun saba yin dogara ga alkawaran Allah. Suna da izni da ikon Almasihu tare da su (Matiyu 28:18).

ne Yesu ya kira su zama almajiransa?

a) Ya kira ma'aikata da masu sana'a su bi shi

b) Ya zapi shugabannin addini

c) Ya karpi kowane mai marmarin binsa

**B. Ka rubuta 'Gaskiya' ko 'Xarya' wajen kowace tambaya**

1. Yesu ya yi ma Yohanna baftisma.
2. Yesu ya warkar da surukar Bitrus.
3. Yesu bai so mutane su ji Labari Mai Daqi ba.
4. Yesu yana gafarta zunubai.
5. Almajiran Yesu sun yi azumi tare da shi.
6. Allah zai yafe ma waqanda suka yi ma Ruhu Mai Tsarki sapo.

***　Yanzu ka karanta Markus 4:1 - 25**

*(Labarin nan kuma yana cikin Luka 8:4 - 15)*

## MISALI MAI SHUKA DA IRI

Yesu ya shiga jirgin ruwa, ya koyar da jama ' a. Idan babu iska, ana jin muryar mutum daga nesa a kan ruwa.

Cikin misalin nan, manomin da ke shukar iri yana kamar da mai yaqa bishara. Iri ya zama kwatancin gaskiyar saxon Allah, wato Labari Mai Daqi. Wanda ke faqin labari, yana Ayafa iri " a cikin duniya. Shi ne mai shuka, ko mashaidi. Mashaidi shi ne wanda yake faqin abin da ya sani ko abin da ya gani.

Manomi yana da iri cikin jakarsa. Yana yafa iri da xarfi sosai (4:4). Kalmomin Yesu suna kamar da iri. Kamar yadda xasa mai kyau ya karpi iri, haka kuma zukata shiryayyu suke karpar gaskiya. Zukatu taurarru ba za su karpi gaskiya ba.

Daga baya Yesu ya bayyana ma almajiransa ma 'a nar misalin:

1. Waqansu zuciyoyi suna da tauri kamar tafarki. Ba su iya karpar Labari Mai Daqi a kan Yesu Almasihu. Xasa mai tauri ce, babu inda iri yake shiga.
2. Wuri mai dutse shi ne kwatancin zukatu waqanda sukan karpi saxon Allah nan da nan, amma suke ja da baya a lokacin wahala. Iri yana tashi da sauri cikin inuwar dutse. Amma xasa ba ta isa ya yi girma ba. Da rana ta yi zafi, sai tsiron ya bushe, ya mutu.
3. Irin da manomi ya shuka wurin xaya yana magana a kan rayuwar da ke cike da abubuwa dabam dabam. An ambaci abokan gaban zuciyar mutum ukku a nan. Sukan halakar da sabon tsiron bangaskiya mai taushi (Matiyu 19:22):
   a) kwaqayin kayan duniya da yawa
   b) xaunar kuqi
   c) neman jin daqi da cin nasara (1 Yohanna 2:2 -16).
4. Irin da aka shuka cikin xasa mai kyau yana kamar da gaskiya wadda zuciya a buqe take karpa. Xasa mai kyau mai zurfi ce, an nome shi don iri ya sami wuri. Yana tashi, yana girma, yana ba da amfani. Amfani ke nan bangaskiya na xwarai ne duk da ayyukan kirki waqanda ke tafiya tare da ita.

Muna shukar iri lokacin da muke gaya ma mutane labarin gaskiyar


Allah, ko lokacin da muka ba wani Littafi Mai Tsarki ya karanta. Waqansu ba za su saurara ba. Waqansu za su ji amma ba za su gane ba. Waqansu za su so su bi Yesu nan da nan, amma za su ja da baya idan akwai matsala, domin bangaskiyarsu ba ta da xarfi. Waqansu za su yi murnar bin Asabuwar hanyar " Yesu, amma sai za su pace saboda kuma suna marmarin hanyoyi dabam dabam.

Yesu ya gargaqar da mutane cewa idan ba su fahimci misalin nan ba, to, da kyar su gane sauran misalai (Markus 4:13). Amma waqanda suka ji suka gane abubuwan nan, za su yi rayuwa masu albarka cikin Mulkin Allah (4:20). Misalin nan ya nuna mana bambanci tsakanin mutane masu ceto da patattu. Ya nuna mana abin da ke faruwa ga mutanen da ba su saurari gaskiyar Allah da kyau ba. Amma mutane da yawa ba za su fahimci abubuwan nan ba.

Yesu yana kamar da fitilla. Sai a Aqaga shi a bisa " domin dukan mutane su ga hasken gaskiyar Allah (Markus 4:22; Yohanna 1:4 - 5). Lokacin da mutane suke kusantowar hasken, sai Ruhu Mai Tsarki yake xara masu haske. Allah zai haskaka hankalunsu idan su gaskanta su dogara gare shi.

## YI MAGANA A KAN WANNAN:

1. Me annabi Ishaya ya ce game da zukata taurararru (Markus 4:12)?
2. Mecece Axasa mai kyau" ?



## Yaqa Labari Mai Daqi

Yesu ya umarci almajirai su koya ma kowa dukan abubuwan da ya koya masu (Matiyu 28:20). Waqansu masu wa 'azi sukan yaqa bishara ta hanyar gaya ma jama' a cewa Allah yake vaunar kowa da kowa, zai kuma albarkaci kowa, ya ba su kyautai masu kyau idan za su bi Yesu. Sukan manta su ce Allah mai tsarki ne, mai vin zunubi. Sukan manta su ce sau da yawa bin Yesu yana da tsada. Yesu ya zo domin ya bayyana cikakkiyar gaskiyar Allah (Yohanna 18:37). Allah ya san yadda muka cancanci hukunci saboda zunubanmu, da yadda muke bukatar samun ¥anci daga zunubanmu. Yesu ya zo domin ya qauki hukuncinmu ta hanyar mutuwa bisa gicciye. Idan mun gaskata wannan, sai an yafe mu an vantar da mu daga zunubanmu, Allah kuma zai karpe mu. Sa' an nan zai ba mu sabon guri cikin wannan rai, duk da bege domin nan gaba, ko da shi ke yana yiwuwa mu sha wuya wani lokaci. Wannan ta zama Bishara cikakkiya wadda muke wa 'azinta muke koyarwa.

Allah yana vaunarka ko da shi ke kana yin laifofi,<br>kana kuma yin mugun tunani.

3. Yaya za mu taimaki iri ya yi girma a zukatan mutane?

* Yanzu ka karanta Markus 4:26 - 34

## MISALAI A KAN BANGASKIYA DA MULKIN ALLAH

Yesu ya yi magana a kan bangaskiya. Dole mutum ya kasance da bangaskiya domin ya gaskanta Allah, ya gamshe shi. Yesu ya yi magana a kan Mulkin Ruhu. Allah ne Sarkin mulkin nan. Bai zama wani mulki wanda sarakunan duniya suka kafa ba. Almajiran Yesu ba su gane abin da yake nufi game da Mulkin Allah ba.

Har yanzu Yesu ya mori misali, ya yi kwatanci da wani abin da suka saba ganinsa sau da yawa. Dole mutum wanda ya shuka iri ya kasance da bangaskiya:

a) Ya kamata ya mori iri na xwarai, ya gaskanta cewa irin nan zai tsira.
b) Ya kamata ya yi haxuri yana jiran iri ya yi girma.
c) Ya kamata ya gaskanta irin zai yi girma da kansa (4:28).
d) Ya kamata ya gaskanta irin zai ba da vava da yawa lokacin girbi (4:29).

Yesu ya faqi wani misali kuma a kan Mulkin Allah. Yana kamar da wata var xaramar xwayar mastad wadda aka shuka cikin lambu. Yana yiwuwa kafin shekara guda ta fi dukan sauran shuke shuken girma, har tsawonta ya kai meta huqu.

Mulkin Allah a duniya ya soma qan xarami. Masu bin Yesu ba su da muhimmanci. Talakawa ne, ba su da wani iko. Amma cikin rayuwarsu, Mulkin Allah ya yaqu ko' ina a sashen duniyan da suka san da ita (Ayyukan Manzanni 1:8; 17:6).

Yau, ana wa 'azin gaskiyar bishara ko 'ina. Sai mutane maza da mata suke xin gaskiyar Allah, ko kuwa suke ba da gaskiya suna samun ceto kuma an haqa su da Ikilisiyar Kirista.

## YI MAGANA A KAN WANNAN:

1. Ta yaya Mulkin Allah yake sa ma xasashen al 'ummai albarka?
2. Yaya Mulkin yake yin girma?
3. Me misalin xwayar mastad yake koya mana a kan Mulkin Allah?
4. Me za mu yi mu taimaki iri yin girma?

## * Yanzu ka karanta Markus 4:35 - 39

(Labarin nan kuma yana cikin Luka 8:22 - 25)

# ALMAJIRAI SUN HAYE TEKU

Yesu ya umarci almajirai su haye zuwa wancan xetaren teku. Lokacin da suke hayewa, hadari ya tashi. Ruwa ya fara shigowar xaramin jirginsu. Almajirai sun ji tsoro saboda hadarin iska, amma Yesu bai ji tsoro ba. Yana barci.

Sun yi kira wurin Yesu cewa, “Malam, za mu halaka, ba ka kula ba ko?” (4:38). Yesu ya tashi zaune. Ya ce wa iska, “Natsu! Ka yi shiru!” Sai iska ya daina, ruwan teku ya kwanta.

Sun dubi junansu, sai suna raqa, “Wane ne wannan? Har iska da ruwan teku ma suna jinsa!” (4:41). Dazu sun ji tsoron hadari, yanzu suna jin tsoron Yesu. Mutum ne, amma ya fi mutum. Shi Allah ne! Yesu ya tambaye su dalilin xaramcin bangaskiyarsu, domin ba su dogara gare shi ya tsare su ba.

Lokacin da zukatanmu suna kamar da haukan ruwan teku ba su kwantawa, Yesu yana gaya mana daidai wannan zancen: ‘Natsu! Ina tare da ku. Ku dogara gare ni.’

*Edité et publié par :* *Imprimé par :*

Da taimakon Allah da gudumawar Kirista a UK da Etats Unis, an buga littafin nan a waqannan vasashe:
Bulgaria, Ethiopie, Inde, Kenya, Malawi, Mongolia, Nigeria, Rwanda, Sudan, Swaziland, da Ouganda.

**Littafin nan yana ba da labarin Yesu, yadda ya fara aikinsa a nan duniya. Yana ba da labarin koyarwarsa, da warkarwar da ya yi, da ma'anar bin Yesu har yau.**

- **Wanene Markus?**
- **Wanene Yohanna Maibaftisma?**
- **Yesu ya zapi almajiransa**
- **Yesu, abokin masu zunubi**
- **Ikon Allah bisa Shaiqan**
- **Al'ajaban Yesu**
- **Warkarwa cikin sunan Yesu**

MANNA PUBLICATIONS suna shirin littattafan fassara na Littafi Mai Tsarki waqanda M. Fred Morris ya rubuta. Tsawon shekaru da yawa, Fred da matarsa Lorna, sun yi tafiye tafiye ko'ina cikin duniya, suna ba da koyarwa da yin wa'azi. Lokacin da suka koma gida suka rubuta waqannan littattafai tare da izni a buga su ko'inda ake bukatar koyarwa Kirista.

ANA AMFANI da littattafan nan domin ka yi bincike kai kaqai, ko tare da xungiya. Za su koya maka gaskiyar Allah. Za su taimake ka ka san Qan Allah, Yesu Almasihu. Za su taimake ka ka shaida bangaskiyarka, da abin da ka sani game da Allah. Za su hana ka zapen mugunyar hanya cikin rayuwarka. Za su gwada maka abin da ke mai kyau, da na mugu. Za su nuna maka abubuwan da Allah yake so, da waqanda yake.